TARE DON
GINA GOMBE
MAFI GIRMA

APC
JAMA'A,
DAMA
DA WADATA.

KUNDIN MANUFOFIN DR. JAMIL ISYAKU GWAMNA
| 2027–2031 |

MANUFOFIN
KAWO SAUYI MAI INGANCI



Dr. Jamil Isyaku
GWAMNA

AYYUKAN YI

INGANTA MASANA'ANTU

BUNKASA ALBARKATUN 'DAN ADAM

SAUYA RAYUWAR KARKARA

GYARA BIRANE

ARZIKIN FASAHAR ZAMANI

INGANTA TSARO

TSARIN SHEKARU HUDU NA SAMAR DA AYYUKA MASU GAMSARWA

ABUBUWAN DA KE CIKI

Alƙawarina ga Al'ummar Jihar Gombe..... 2
Burina 3
Tsarin Gudanarwa 4
Ginshiƙai Bakwai na Manufofin Kawo Sauyi Mai Inganci..... 4
Aiwatarwa da Bin diddigi 5
Manyan Manufofin Shekaru Huɗu 5

Ginshiƙi na 1: Ababen More Rayuwa da Muhimman Ayyukan Al'umma 7
Ginshiƙi na 2: Bunƙasa Masana'antu 10
Ginshiƙi na 3: Taimakon Jama'a da Albarkatun Ɗan Adam..... 12
Ginshiƙi na 4: Noma da Sauya Rayuwar Karkara 17
Ginshiƙi na 5: Kasuwanci, Cinikayya da Yawon Bude Ido..... 20
Ginshiƙi na 6: Fasahar Zamani da Shigar Kowa Cikin Tattalin Arzikin Dijital.. 24
Ginshiƙi na 7: Inganta Tsaro da Muhalli..... 27

Falsafar Gudanar da Mulkinmu..... 31
Tsarin Bin Diddigi 32
Alƙawarina na Kaina..... 33
Kammalawa..... 34

Alƙawarina ga Al'ummar Jihar Gombe

Wannan kundin manufofi wata muhimmiyar yarjejeniya ce ta alƙawari tsakanina da nagartattun al'ummar Jihar Gombe.

Na fahimci cewa mulki ba wata alfarma ba ce, illa amana mai girma da ake samu ta hanyar hidima, a tabbatar da ita ta hanyar aiwatarwa, sannan a sabunta ta ta hanyar yin aiki cikin gaskiya da rikon amana.

Na kuma fahimci cewa Jihar Gombe a yau tana cin gajiyar gagarumin aikin jagoranci na Mai Girma Gwamna Muhammadu Inuwa Yahaya, CON (Dan Majen Gombe), wanda ya sauya yadda ake kallon yiwuwar ci gaba a jiharmu. Daga gine-gine da ababen more rayuwa zuwa ilimi; daga kiwon lafiya zuwa muhalli; daga gyaran tsarin ma'aikatan gwamnati zuwa jawo zuba jari; daga zaman lafiya da tsaro zuwa samun karɓuwa a duniya, Gwamna Inuwa ya shimfiɗa ingantaccen tubalin ci gaba.

Ban zo domin in sake ƙirƙirar abin da aka riga aka fara ba. Na zo ne domin tabbatar da cewa ayyukan ci gaba sun ci gaba da tafiya, kuma kowa ya amfana da su.

Tsarinmu na ginshiƙai bakwai, mai suna "Manufofin Kawo Sauyi Mai Inganci", ba taken yaƙin neman zaɓe kawai ba ne. Tsari ne na aiki wanda za a iya auna nasarorinsa, mai yiwuwa a aiwatar, kuma wanda ya dogara da ainihin buƙatun al'ummarmu.

Idan aka zaɓe ni Gwamna, zan yi amfani da gogewata a ɓangarorin gwamnati da kamfanoni masu zaman kansu, da alaƙoƙina na ƙasa da ƙasa, da kuma albarkatun ɗan Adam da na ƙasa da Jihar Gombe ke da su, domin ɗaga jiharmu zuwa matsayi mafi girma na bunƙasar tattalin arziki da zamantakewa.

Ina gayyatar kowane ɗan Jihar Gombe da duk masu ruwa da tsaki su karanta wannan kundin, su tattauna shi, su yi tambayoyi, sannan su ba mu amanar aiwatar da shi.

Sa hannu:
Dr. Jamil Isyaku Gwamna



Manufa ta (My Vision)

Gombe Mai Wadata, Tsaro da Haɓakar Ayyukan Samar da Arziki ga Kowa

Jihar Gombe tana wani muhimmin mataki na yanke shawarar makomarta. Al'ummarmu masu ƙwazo ne; matasanmu na da basira; manomanmu na da juriya; 'yan kasuwarmu kuma na da himma. Duk da haka, har yanzu ba a yi cikakken amfani da damar tattalin arziki da albarkatun ɗan Adam na jihar ba.

Wannan kundin manufofi zai taimaka wajen mayar da Gombe:

- Babbar cibiyar masana'antun sarrafa amfanin gona da harkokin sufuri da rarraba kaya a Arewacin Najeriya.
- Fitacciyar cibiyar taruka, yawon buɗe ido, karɓar baƙi da al'adu a Arewacin Najeriya.
- Cibiyar kirkire-kirkiren fasahar zamani wadda matasa ke jagoranta.
- Jihar da kowane yaro zai samu ilimi a makaranta mai aminci.
- Jihar da ruwa, tsaftar muhalli, magudanan ruwa da kariya daga zaizayar ƙasa ke kare rayuka da mutuncin jama'a.
- Jihar da ayyukan yi, kasuwanci, yawon buɗe ido, karɓar baƙi da ci gaban da ya haɗa kowa za su isa ga kowane gida.





Tsarin Gudanarwa (Administrative Scope)

A cikin wannan kundin, “LGA” na nufin ƙananan hukumomin jihar, yayin da “LCDA” ke nufin yankunan ci gaban ƙananan hukumomi da dokar Majalisar Dokokin Jihar Gombe ta kafa. Duk wani alƙawarin da aka ware wa LCDA za a tsara shi, a yi masa kasafi, a aiwatar da shi, sannan a bayar da rahoton sa a matakin LCDA bisa dokokin jihar da tsarin gudanarwa da ya dace.

Manufofin Kawo Sauyi Mai Inganci (IMPACTS)

Wannan suna yana bayyana ginshiƙai bakwai na tsarin ci gaban Jihar Gombe. Kowane ginshiƙi yana ƙunshe da alƙawura bayyanannu, manufofin da za a iya aunawa, lokutan aiwatarwa, da hanyoyin bayyana sakamako ga jama’a.

1. **ABABEN MORE RAYUWA DA MUHIMMAN AYYUKAN JAMA’A**
   Kammalawa, kulawa, faɗaɗawa da gina sababbin ayyuka.

2. **MASANA’ANTU DA BUNKASA SARRAFA KAYAYYAKI**
   Daga gonaki zuwa masana’antu; daga Gombe zuwa kasuwannin duniya.

P. **CI GABAN JAMA’A DA ALBARKATUN ƊAN ADAM**
   Habaka ilimi, Inganta Kiwon Lafiya, ƙwarewa da damar jama’a.

A. **NOMA DA SAUYA RAYUWAR KARKARA**
   Ciyar da ƙasa da inganta hanyoyin samun abin dogaro a karkara.

C. **KASUWANCI, CINIKI DA YAWON BUƊE IDO**
   Tallafa wa ’yan kasuwa, mata da matasa.

T. **FASAHAR ZAMANI DA SHIGAR KOWA CIKIN TATTALIN ARZIKIN DIJITAL**
   Kai Gombe zuwa mataki mai girma a ci gaban fasahar zamani.

S. **TSARO DA KULA DA MUHALLI**
   Kare rayuka, dukiyoyi, hanyoyin samun abin dogaro da muhalli.

Aiwatarwa da Bayar da Bayani ga Jama'a (Implementation & Accountability)

Za mu mayar da kowane alƙawari zuwa tsarin aiki na kowace shekara, tare da bayyana ma'aikata ko hukumar da ke da alhakin aiwatarwa, kasafin kuɗin da aka amince da shi, bayanan ma'aunin farko, matakan nasara na shekara-shekara, da jadawalin sanar da jama'a.

Za mu wallafa rahotannin ci gaba ta hanyar tsarin bibiyar ayyukan gwamnati da jama'a za su iya gani. Za a tabbatar da manyan sakamako ta hanyar tantancewa mai zaman kanta, tare da yin bitar tsakiyar wa'adi domin gano jinkiri, gyara hanyoyin aiwatarwa, da kare manyan manufofin kundin.


Manyan Manufofin Shekaru Hudu (Headline 4-Year Targets)

A ƙarshen wa'adinmu na shekaru huɗu, zuwa shekarar 2031, muna shirin samar da sababbin ayyukan yi 100,000 a dukkan ɓangarori, ba tare da ƙirga aiki guda sau biyu ba, tare da bayar da rahotanni bisa kowane fanni.

A cikin wannan adadi, za mu samar da:

Ayyukan yi kai tsaye **10,000** a masana'antu.





Ayyukan yi **50,000** na kaikaice a masana'antu da hanyoyin samarwa da rarraba kayayyaki.

Ayyukan yi **20,000** na kai tsaye da na kaikaice a fannin kiwon dabbobi da sarrafa kayayyakinsu.



Bugu da ƙari,



Za mu kafa rukunan noma 110 da ƙungiyoyin haɗin gwiwar kiwo da madara 100.



Mu tallafa wa ƙananan da matsakaitan sana'o'i 50,000.



Mu samar da cibiyoyin masana'antu ko sarrafa amfanin gona guda uku masu muhimman ababen more rayuwa.



Mu samar ko sauƙaƙa samun gidaje masu araha ko filayen gini masu kayan more rayuwa guda 10,000.



Mu kula da inganta ɓangarorin kiwon lafiya na matakin farko guda biyu a kowace mazaba;

sannan mu wallafa rahotannin auna ci gaba kowane wata uku.



GINSHIKI NA 1: ABUBUWAN MORE RAYUWA DA MUHIMMAN AYYUKAN AL-UMMA

Babbar Manufa:

Kammala ayyukan da ake yi, kula da kadarorin da ake da su, faɗaɗa muhimman ayyukan hidima, da gina kayayyakin more rayuwa da Gombe ke buƙata.

1.1 Kammala Ayyukan da ake yi da ƙaddamar da sababbi

Za mu kammala dukkan ayyukan tituna, gadoji, fitilun tituna masu amfani da hasken rana da sauran ayyukan more rayuwa da gwamnatin Gwamna Inuwa Yahaya ta fara, bisa jadawalin da aka tsara.

1.2 Haɗa Al'ummomin Karkara da Hanyoyin Sufuri

- Shirin Network 11/100 2.0 zai gina ƙarin kilomita 1000 na hanyoyi bisa buqatun kowace LCDA, ya tabbatar da cewa hanyoyi masu kwalta sun haɗa kowace LCDA, tare da samar wa kowace al'ummar manoma hanyar mota zuwa kasuwa mafi kusa.
- Za mu yi haɗin gwiwa da Gwamnatin Tarayya da cibiyoyin bayar da kuɗaɗen raya ƙasa domin samun tallafin faɗaɗa hanyoyin karkara.

1.3 Gidaje da Sabunta Birane

- Za mu samar ko taimaka wajen samar da aƙalla gidaje masu araha **10,000** ko filayen da aka tanadar musu da ayyukan more rayuwa zuwa 2031, ta hanyar filaye masu cigaban zamani, rabon fili na gaskiya, tallafin jinginar gida, tsarin haya-da-mallaka, gidajen haɗin gwiwa, ƙa'idojin jure sauyin yanayi da haɗin gwiwar gwamnati da kamfanoni. Za a ba iyalai masu ƙaramin da matsakaicin ƙarfi, ma'aikata, gidajen da mata ke jagoranta da masu nakasa fifiko.
- GOSUPDA da GOGIS za su tabbatar da aiwatar da umarnin zartarwa kan Yankin Raya Babban Birnin Gombe.
- Za mu gina ƙarin titunan cikin gari, musamman a unguwannin gefen Gombe, domin rage cunkoso da haɗa al'ummomi.
- Za mu kammala aikin titin zagaye na arewacin Gombe, sannan mu sake ginawa da faɗaɗa titin zagaye na kudancin Gombe.
- Za mu samar da wuraren shakatawa na jama'a a kowace LCDA.
- Za mu raya da kula da wuraren shakatawa, bakin ruwa, cibiyoyin nishaɗi da wuraren baƙi domin inganta rayuwa da bunƙasa yawon buɗe ido.



1.4 Hukumar Kula da Kayayyakin More Rayuwa da Gine-ginen Gwamnati

- Za mu kafa hukuma ta musamman domin kula da tituna, fitilun tituna, gine-ginen jama'a da sauran kayayyakin more rayuwa da ake da su.

1.5 Ruwa da tsaftar muhalli

- Za mu kammala aikin samar da ruwan sha na yankin Gombe da ake yi, tare da sake fasalin Hukumar Ruwa ta Gombe domin inganta hidimarta.
- Za mu gina ko gyara rijiyoyin burtsatse 50 a kowace LCDA cikin shekaru huɗu.
- Za mu wallafa tsarin rijiyoyin burtsatse na kowace shekara a matakin LCDA, wanda zai bayyana jimillar jihar, rabon kowace LCDA da ma'aunin yawan jama'a, matsugunai da samun ruwa; za a rika bayar da rahoton kammalawa da aiki.
- Za mu gina ƙarin wuraren zubar da shara a dukkan mazabu 114.
- Za mu ɗauki jami'an sa ido kan tsafta domin kiyaye tsaftar Gombe.
- Za mu haɗa gwiwa da kamfanoni domin samar da cibiyar sarrafa shara da sake amfani da ita a birnin Gombe.

1.6 Manufofin Ruwa da Tsaftar Muhalli

Zuwa 2031:

- Za mu ƙara yawan jama'ar da ke samun ruwa mai ɗorewa a garuruwan da aka fi bai wa fifiko da aƙalla kashi 50% idan aka kwatanta da matakin 2027.
- Za mu cim ma matsakaicin samar da ruwa na aƙalla sa'o'i 12 a rana a yankunan da tsarin ya rufe, gwargwadon ƙarfin tsarin da aka tabbatar.
- Za mu rage ruwan da ba a samun kuɗin shiga daga gare shi da aƙalla kashi 25%.
- Za mu tantance da taswira dukkan manyan wuraren barazanar zaizayar ƙasa da ambaliya.
  Za mu daidaita ko gyara aƙalla manyan ramukan zaizayar ƙasa 10 masu haɗari da hanyoyin magudanar ruwa 20 da aka fifita.
  Za mu rage maimaituwar barnar ambaliya da zaizayar ƙasa ga muhimman kadarorin jama'a da aƙalla kashi 50%.



1.7 Sufuri da Makamashi

- Za mu haɗa gwiwa da masu zuba jari wajen gina tashar samar da wutar lantarki mai ƙarfin megawatt 100 ta hasken rana domin wadatar masana'antu da gidaje da wutar da ba ta dogara ga babban layin ƙasa ba.
- Za mu samar da motocin bas masu amfani da lantarki domin zirga-zirga a birnin Gombe da bas masu amfani da iskar gas CNG domin haɗa manyan garuruwa.
- Za mu samar da tashoshin cajin motocin lantarki da cika CNG a birnin Gombe da hedikwatar kowace LCDA.
- Za mu gina titunan cikin gari da fitilun titi masu amfani da hasken rana domin sauƙaka zirga-zirga, inganta tsaro da muhalli.
- Za mu inganta hanyoyin shiga, alamomin hanya, hasken titi da kayayyakin more rayuwa na wuraren yawon buɗe ido kamar Dam ɗin Dadin Kowa, tsaunukan Tula, Tangale da Kilang, kwarin Cham da sauran wuraren da aka ware.

1.8 Muhimman Ayyukan More Rayuwa na Yankin Arewa Maso Gabas

- Za mu yi aiki da Gwamnatin Tarayya da jihohin maƙwabta wajen faɗaɗa hanyar Abuja–Akwanga–Jos–Bauchi–Gombe zuwa hanyoyi biyu a kowane ɓangare.
- Za mu tallafa wa aikin babbar hanyar Gombe–Biu.
- Za mu inganta hanyar Gombe–Bajoga–Nafada da hanyar Gombe–Dukku–Darazo.
- Za mu inganta ayyukan layin dogo, jigilar wutar lantarki da intanet mai sauri na yankin Arewa maso Gabas, domin haɗin kan tattalin arziki da farfaɗowa bayan rikice-rikice.





GINSHIKI NA 1: ABUBUWAN MORE RAYUWA DA MUHIMMAN AYYUKAN AL-UMMA

Babbar Manufa:
Sauya tsarin fitar da ɗanyen albarkatu zuwa fitar da kayayyakin da aka sarrafa ko aka kammala ƙera su.

2.1 Injinan Noma da Sarrafa Amfanin Gona

- Za mu kammala kuma mu fara gudanar da ayyuka a Yankin Musamman na Raya Noma da Kiwo.
- Za mu yi amfani da matsayin Gombe a shirin SAPZ domin cin gajiyar damar da ke cikin dukkan matakan kasuwancin noma.
- Za mu tallafa da faɗaɗa rukunin ƙananan masana'antun sarrafa amfanin gona na Gombe, kamar injinan shinkafa da matatun mai, ta hanyar makamashi, injuna na zamani da wuraren aiki na haɗin gwiwa.

2.2 Farfaɗo da Masana'antu

- Za mu kammala kuma mu fara amfani da mataki na biyu na Filin Masana'antu na Muhammadu Buhari a matsayin ɗaya daga cikin aƙalla rukunan masana'antu ko sarrafa amfanin gona guda uku da za su fara aiki zuwa 2031. Kowannensu zai kasance da ingantacciyar wuta, titunan ciki, ruwa, magudanar ruwa, tsaro, kula da shara da tallafin kasuwanci.
- Za mu haɗa gwiwa da masu zuba jari wajen samar da tashar wutar hasken rana mai ƙarfin megawatt 100 domin masana'antu da gidaje.
- Za mu tallafa wa masana'antu da ƙanana da matsakaitan kasuwanci ta rance, tallafi da horo domin ƙara ƙarfin gasa.
- Za mu tuntubi Gwamnatin Tarayya domin dorewar binciken man fetur a Kolmani.

2.3 LGA ɗaya, Samfuri ɗaya: Daga ƙwarewar gida zuwa kasuwar duniya

- Kowace LCDA za ta gano kuma ta raya wani fitaccen samfuri guda ɗaya bisa fa'idar da take da ita, ƙwarewar jama'a, samuwar albarkatun ƙasa, buƙatar kasuwa da kiyaye muhalli.
- A cikin shekara ta farko, za mu wallafa taswirar samfuran LCDAs da tsarin aiwatarwa na shekaru huɗu, wanda zai nuna yawan samarwa, hukumomin da ke da alhaki, kayayyakin more rayuwa, kuɗaɗen da ake buƙata da ayyukan yi da ake sa ran samu.



- Za mu haɗa manoma, masu sana'o'in hannu, masu sarrafa kayayyaki, mata da matasa 'yan kasuwa cikin ƙungiyoyin haɗin gwiwa masu gaskiya da rukunan sana'o'i.
- Za mu samar da wuraren ƙera da sarrafawa na haɗin gwiwa, wuta, ruwa, ma'ajiya, gwajin inganci, marufi, sufuri da damar shiga kasuwannin intanet bisa buƙatar kowane samfuri.
- Za mu samar da wata hanyar tallafin kuɗi da za ta haɗa tallafin kyauta, rance mai sauƙi, hayar injuna da jarin kamfanoni, tare da bayyanannun ka'idoji domin hana siyasantar da tallafin.
- Za mu taimaka wa masu samarwa wajen cika ka'idojin takardar shaida, aminci, alamar kasuwanci da bibiyar asalin kaya, tare da haɗa su da sayayyar gwamnati, manyan masu saya, kasuwannin intanet, baje koli da damar fitar da kaya.
- Za mu tabbatar da shigar mata, matasa da masu nakasa ta hanyar horo, koyon sana'a, tallafin kasuwanci da adalci wajen samun kayan aiki.
- Za mu wallafa rahoton sakamakon kowace LCDA a kowace shekara, wanda zai nuna jarin gwamnati, yawan samarwa, bunƙasar kasuwanci, ayyukan yi, jarin kamfanoni da ƙaruwar kuɗin shiga na gidaje.

2.4 Manufofin Samar da Ayyukan yi a Masana'antu

Zuwa 2031:

- Za mu samar da ayyukan yi kai tsaye 10,000 a masana'antu da ayyuka 50,000 na kaikaice a masana'antu da sarƙar samar da kayayyaki, bisa tsarin ƙididdiga da aka wallafa domin kauce wa maimaita lissafi.
- Za mu cim ma hakan ta hanyar fara gudanar da ayyuka a Cibiyar Noma da Masana'antu ta Renewed Hope, mataki na biyu na Filin Masana'antu na Muhammadu Buhari, ɓalla rukunan masana'antu ko sarrafa amfanin gona guda uku, da shirin LCDA ɗaya, samfuri ɗaya.
- Za mu fifita ayyukan sarrafa amfanin gona, abinci, fata, marufi, ajiya, ƙera kayan aiki, gyaran injuna, tabbatar da inganci, makamashin masana'antu, sufuri da sarƙoƙin samar da kayayyaki.
- Za mu danganta tallafin kuɗi, injuna, makamashi, horo, koyon sana'a da damar kasuwa da tabbataccen samarwa da riƙe ayyukan yi.
- Za mu wallafa rahotannin kwata-kwata kan ayyukan yi kai tsaye da na kaikaice da aka samar kuma aka dore da su, kamfanonin da aka tallafa, matsayin ayyuka, jarin da aka jawo da ci gaban cim ma burin ayyuka 60,000.



GINSHIKI NA 3: JAMA'A DA INGANTA ALBARKATUN ƊAN ADAM

Babbar Manufa:
Kowane yaro ya samu ilimi, kowace uwa ta samu kariya, kowane matashi ya samu ƙwarewa, kuma kowace mace ta samu damar dogaro da kai.

3.1 Ilimi

- Ɗaukar malamai da horar da waɗanda ake da su: Za mu ɗauki sababbin malamai 1,000 tare da horar da malamai 10,000 a shekaru na 1–2.
- Mayar da yaran da ba sa makaranta cikin aji: Za mu shigar da yara 100,000 a kowace shekara, wato 400,000 cikin shekaru huɗu, tare da rahoton shekara-shekara da zai bambanta sababbin ɗaliban da aka shigar da waɗanda aka ci gaba da rikewa.
- Karin babbar makarantar sakandare guda ɗaya a kowace shiyyar sanata: Za mu gina manyan makarantun sakandare guda uku, ɗaya a kowace shiyya, a shekaru na 2–3.
- Farfaɗo da makarantun fasaha da koyon sana'a a dukkan shiyyoyi uku, da bunƙasa ilimin amfani da fasahar dijital a makarantun firamare da sakandare; a cim ma kashi 90% na ƙwarewar dijital zuwa 2030, a shekaru na 2–3.
- Ilimin dijital a dukkan makarantun sakandare: Manufar ɗaukar mataki a kashi 100% na makarantun, zuwa shekara ta 4.
- Tallafin karatu da manyan makarantu: Za mu ba da tallafin karatu bisa buƙata, tare da samar da tsarin kuɗaɗen da zai dore ga manyan makarantun jihar, a shekaru na 1–4.

3.2 Manufofin Ilimi

Zuwa 2030:

- Za mu inganta aƙalla kashi 60% na makarantun gwamnati na matakin ilimin bai ɗaya.
- Za mu horar, jagoranta ko ba da takardar ƙwarewa ga aƙalla malamai 10,000; shirin zai kai ga aƙalla kashi 80% na adadin malaman da aka tabbatar a 2027, tare da ƙara adadin da ake buƙata idan ya zama dole.
- Za mu inganta sakamakon karatu, rubutu da lissafi da aƙalla kashi 35% bisa matakin 2027.
- Za mu ba aƙalla ɗalibai 10,000 daga iyalai marasa ƙarfi tallafin karatu a manyan makarantu.



- Za mu ɗauki nauyin karatun aƙalla ɗalibai 3,000 a muhimman fannoni bisa sharadin yin hidima bayan kammala karatu.
- Za mu samar da abincin makaranta ga aƙalla yara 250,000 daga iyalai marasa ƙarfi.
- Za mu tallafa wa aƙalla gidaje 200,000 masu rauni ta shirye-shiryen kariyar zamantakewa da suka shafi ilimi, lafiya, ƙwarewa, abinci ko hanyoyin samun kuɗin shiga.

3.3 Kiwon Lafiya

- Kula da cibiyoyin kiwon lafiya na matakin farko guda biyu a kowace mazaba: Za mu tabbatar da cewa aƙalla cibiyoyi biyu masu cikakken aiki da kayan aiki suna ba da hidima a kowace mazaba, har da hidimar sa'o'i 24; za a gina ƙarin cibiyoyi ne kawai idan binciken buƙata ya nuna gibin yawan jama'a, nisa ko ƙarfin hidima. Lokaci: shekaru na 1–2.
- Manyan asibitoci: Za mu inganta ko gina babban asibiti guda ɗaya a kowace shiyyar sanata, jimilla uku. Lokaci: shekara ta 2.
- Shirin Lafiyar Uwayen Gombe: Za mu ba da kulawar ciki, haihuwa da bayan haihuwa kyauta. Lokaci: shekara ta 1.
- Ma'aikatan lafiya: Za mu ɗauki likitoci, nas-nas, ungozomomi, masana harhaɗa magunguna da sauran ma'aikatan lafiya 500, musamman a yankunan karkara. Lokaci: shekaru na 1–2.
- Inshorar lafiya ga kowa: Za mu faɗaɗa Go-Health zuwa masu cin gajiyar shirin miliyan ɗaya. Lokaci: shekaru na 1–4.

3.4 Karfafa Matasanmu

- Asusun Tallafin Kasuwancin Matasan Gombe: Za mu ba matasa masu shekaru 18–35 rance mai ƙarancin ruwa, ƙasa da kashi goma cikin ɗari, da tsarin biya mai sassauci.
- Cibiyoyin koyon sana'a: Za mu kafa guda ɗaya a kowace shiyyar sanata, domin koyar da ICT, ɗinki, girki, gyaran gashi, walda da sauran sana'o'i.
- Za mu horar da tallafa wa matasa 5,000 a kowace shekara ta shirye-shiryen sana'a da kasuwanci, ba tare da haɗa su da adadin masu horon dijital na G-ODA ba. Za mu bayar da rahoto daban kan waɗanda suka kammala, koyon aiki, tallafin kasuwanci da ayyukan yi.







- Za mu horar da tallafa wa matasa 5,000 a kowace shekara ta shirye-shiryen sana'a da kasuwanci, ba tare da haɗa su da adadin masu horon dijital na G-ODA ba. Za mu bayar da rahoto daban kan waɗanda suka kammala, koyon aiki, tallafin kasuwanci da ayyukan yi.



- Za mu ware kashi 40% na damar shiga harkokin mulki ga matasa.
- Za mu tallafa wa matasa su shiga yawon buɗe ido, karɓar baki, nishaɗi, sana'o'in al'adu da shirya taruka ta hanyar horo da tallafin kasuwanci.



3.5 Harkokin Ɗalibai

- Za mu biya kuɗin jarrabawar NECO, WAEC da JAMB ga dukkan ɗaliban ajin ƙarshe na sakandare.
- Za mu sake duba kuma mu ƙara tallafin karatun ɗalibai domin ya dace da halin tattalin arziki.



- Za mu sake duba tare da rage kuɗin makaranta da rajista ga 'yan asalin Gombe a manyan makarantun jihar.
- Za mu haɗa gwiwa da cibiyoyin da suka dace domin tallafin karatu a ƙasashen waje bisa ƙwarewa da buƙata.



- Za mu ɗauki nauyin karatun aƙalla ɗalibai 3,000 da suka cancanta daga iyalai marasa ƙarfi a fannonin lafiya, ilimi, injiniya, noma da fasaha, ta tsarin zaɓe mai gaskiya da sharadin yin aiki a Gombe bayan kammala karatu.

3.6 Mata, Yara da Iyali

- Shirin Karfafa Tattalin Arzikin Mata: Za mu samar da horo, tallafin kuɗi da rance, da damar kasuwa ga mata 10,000 kai tsaye cikin shekaru huɗu.
- Za mu ware rumfunan kasuwa ga mata a dukkan kasuwannin da aka sabunta.
- Za mu ware kashi 35% na naɗe-naɗen gwamnati ga mata.

- Gina jiki ga uwa da yaro: Za mu yaki gajeriyar girma da tsananin rama sakamakon rashin abinci mai gina jiki, ciki har da rarraba abincin warkarwa na musamman (RUTF) ga yara.
- Ilimin ’ya’ya mata: Za mu ƙara yawan ’yan mata a makarantu da rage tazarar jinsi.
- Za mu gina ko inganta makarantar sakandaren kwana ta ’yan mata kaɗai guda ɗaya a kowace LCDA, tare da kayan aiki.
- Jin daɗin iyali: Za mu samar da tsarin kiwon lafiya da kariyar zamantakewa da ya dace da buƙatun iyalai.



- Za mu kafa cibiyoyin horar da ma’aikatan karɓar baki da yawon buɗe ido tare da kamfanoni da cibiyoyin ilimi.
- Za mu tallafa wa bukukuwan al’adu, zane-zane, sana’o’in hannu, fina-finai, tufafi da gadon al’adu domin bunƙasa yawon buɗe ido da ayyukan matasa.
- Za mu tallata Gombe a matsayin wurin wasanni, nishaɗin waje, taruka da baje-kolin al’adu.

3.7 Wasanni, Nishaɗi da Sana’o’in Kirƙira



- Za mu gina cibiyoyin wasanni da nishaɗi a kowace LCDA.
- Za mu kafa Kamfanin Gudanar da Wasannin Gombe domin gano baiwa da jawo jari.
- Za mu sake fasalin Gombe United FC da sauran ƙungiyoyin wasanni na jihar domin inganta nasara.
- Za mu ba masana’antun ƙirƙira tallafi na musamman domin bunƙasa baiwar matasa.



3.8 Gyaran Ma'aikatan Gwamnati

- E-Governance: Support transition to E-governance and digital workflows.
- Training and Capacity Building: Provide targeted training and capacity-building opportunities for civil servants to increase productivity and welfare.
- Promotion and Benefits: Ensure timely promotions and the prompt payment of salaries, pensions, gratuities, and other approved benefits.

3.9 Mutane Masu Buƙatu na Musamman

- Za mu ƙarfafa Hukumar Masu Nakasa ta Jihar Gombe domin ƙara shigar masu nakasa cikin mulki.
- Za mu tallafa musu da ƙwarewa, sana'o'i da hanyoyin samun kuɗin shiga domin dogaro da kai da rage bara.
- Za mu ba masu nakasa inshorar lafiya kyauta ta Go-Health.
- Za mu gina ko inganta makarantun masu buƙatu na musamman a kowace shiyyar sanata.



3.10 Manufofin Hidimar Jama'a

Zuwa 2031:

- Za mu mayar da akalla hidimomin gwamnati 20 da ake yawan nema zuwa tsarin dijital.
- Za mu warware akalla kashi 70% na korafe-korafen jama'a da aka yi rajista cikin wa'adin da aka amince da shi.
- Za mu mayar da bayanan ma'aikata zuwa dijital kuma mu horar da akalla kashi 80% na ma'aikatan gwamnati a fannonin hidima, dijital, ɗabi'a da auna aiki.
- Za mu kammala tantance dukkan haƙƙoƙin ritayar da ba a biya ba a shekara ta 1, mu fara biya a matakai a shekara ta 2, sannan mu rage bashin da aka tabbatar da akalla kashi 80% zuwa 2030.
- Za mu tabbatar da akalla kashi 10% na masu cin gajiyar shirye-shiryen ƙwarewa, ƙananan kasuwanci, gidaje, tallafin karatu da kariyar zamantakewa sun fito daga masu nakasa ko wasu rukunin jama'a masu rauni.



GINSHIKI NA 4: NOMA DA SAUYA RAYUWAR KARKARA

Babbar Manufa:
Expand mechanisation, increase yields, reduce post-harvest losses, and strengthen rural economies.

4.1 Ban-ruwa da Noman Rani





- Za mu faɗaɗa shirye-shiryen ban-ruwa a madatsun Dadin Kowa, Balanga da Cham, da yankunan rafin Dadinkowa a ƙananan hukumomi huɗu: Yamaltu/Deba, Funakaye, Nafada da Dukku.
- Za mu gina ƙananan madatsun ruwa na ƙasa a sassan jihar domin ban-ruwa, kiwon dabbobi da adana ruwa lokacin fari.
- Za mu rage wa manoman rani farashin famfunan ruwa, iri da taki ta tallafi.
- Za mu samar da injinan noma da hidimar jami'an faɗakarwa ta Go-Tech Innovation Hub da Kwalejin Noma ta Jami'ar Jihar Gombe (GSU).

4.2 Manufofin Samar da Amfanin Gona

- Za mu ƙara matsakaicin yawan amfanin manyan gonaki kamar masara, gero, wake, dawa da shinkafa da aƙalla kashi 25% daga matakin 2027 da aka tabbatar, zuwa 2030. Za mu rika bayar da rahoto kan yawan amfanin gona, faɗin ƙasar noma, kadadar ban-ruwa da asarar bayan girbi.

Zuwa 2031:

- Za mu kafa aƙalla rukunan haɗin gwiwar noma 110 masu aiki a dukkan ƙananan hukumomi 11.
- Za mu ƙara matsakaicin amfanin gonakin da aka fifita da aƙalla kashi 25% daga matakin 2027.
- Za mu faɗaɗa gonakin da ake ban-ruwa kuma suke aiki da aƙalla kashi 35%.



- Za mu rage asarar bayan girbi da kashi 25%.
- Za mu tallafa wa aƙalla manyan ko matsakaitan cibiyoyin sarrafa amfanin gona guda takwas.
- Za mu ƙara kuɗin shigar manoman da suka shiga shirin da kashi 25%, tare da tabbatar da cewa mata da matasa sun kai aƙalla kashi 40% na mahalarta.

4.3 Kayayyakin More Rayuwa Bayan Girbi

- Ɗakunan ajiya masu sanyi: Za mu samar da su a dukkan manyan al'ummomin noma a shekaru na 1–2.
- Filayen busar da tumatir, barkono da makamantansu: Za mu samar da su a al'ummomi 100 a shekara ta 1.
- Hanyoyin jigilar amfanin gona na karkara: Za mu ba wuraren da ake yawan girbi fifiko a shekaru na 1–3.
- Tsarin bayanan kasuwa: Za mu ba manoma bayanan farashi da buƙatar kasuwa a kan lokaci a shekaru na 1–4.
- Kananan cibiyoyin kuɗi na karkara: Za mu haɗa gwiwa da kamfanonin fasahar kuɗi domin tallafa wa bankunan ƙananan rance na karkara, da faɗaɗa samun rance da inshora ga kayan noma a shekaru na 1–4.

4.4 Injinan Noma da Faɗakar da Al-umma

- Za mu ɗauki jami'an faɗakarwa na noma 300, mu tura su al'ummomin manoma.
- Za mu kafa gonakin gwaji a kowace LCDA domin horon aiki kai tsaye.
- Za mu ƙaddamar da hidimar shawarwari ta wayar hannu kan yanayi, kwari da cututtuka, da farashin kasuwa.
- Za mu kafa cibiyoyin injinan noma a kowace LCDA, da taraktoci, jiragen sama marasa matuƙi (drones) da sauran kayan aiki da manoma za su iya haya.

4.5 Zamanantar da Kiwo

- Za mu kafa Ma'aikatar Raya Kiwo domin cin gajiyar dukkan matakan sarƙar kiwo, ciki har da kiwon shanu domin ƙiba, sarrafa madara da samar da fata.
- Za mu kammala kuma mu fara aiki a Yankin Musamman na Raya Noma da Kiwo da gwamnatin Gwamna Inuwa Yahaya ke ginawa.
- Za mu gina hanyoyin ruwa a Wurin Kiwo na Wawa-Zange, mu raya shi zuwa yankunan kiwo na zamani masu wuraren shayar da dabbobi da asibitocin dabbobi.



4.6 Manufofin Zamanantar da Kiwo

Zuwa 2031:

- Za mu raya ko inganta aƙalla muhimman yankunan hidimar kiwo guda shida.
- Za mu tallafa wa ƙungiyoyin haɗin gwiwar madara da masu samarwa 100 masu aiki.
- Za mu ƙara yawan dabbobin da ke samun hidimar lafiya da na likitocin dabbobi da kashi 30% bisa matakin 2027.
- Za mu ƙara tattara madara ta tsarin kasuwanci na hukuma da shiga kasuwar madara da aƙalla kashi 25%.
- Za mu zamanantar da wuraren yankan dabbobi, sarrafa nama ko kasuwannin dabbobi guda huɗu.
- Za mu tallafa wa samar da aƙalla ayyukan yi 20,000 kai tsaye da na kaikaice a sarƙar kasuwancin kiwo.

4.7 Yawon Buɗe Ido na Noma da Kasuwancin Karkara

- Za mu tallata yawon gonaki, baje-kolin dabbobi, bukukuwan noma da bukukuwan abinci a matsayin ƙarin hanyoyin samun kuɗin shiga ga karkara.
- Za mu tallafa wa sana'o'in yawon buɗe ido na al'umma a kusa da madatsu, dazuzzuka, wuraren kiwo da wuraren tarihi da al'adun karkara.
- Za mu ƙarfafa tallata amfanin gona na gida, abincin gargajiya da sana'o'in hannu ta sarƙar kasuwancin yawon buɗe ido.

4.8 Magance Rikicin Manoma da Makiyaya

- Za mu kafa majalisun sulhu a kowace LCDA da rikicin ya shafa, tare da wakilan manoma, makiyaya da shugabannin al'umma.
- Za mu maido da hanyoyin kiwo, wuraren kiwo da gandun daji, tare da ba su kariya.
- Za mu kare manoma da makiyaya: ba za mu ɗauki dukkan makiyaya a matsayin masu laifi ba, amma za a tabbatar da hukunci da biyan diyya idan wani makiyayi ya kutsa gona ko ya lalata amfanin gona.



GINSHIKI NA 5: KASUWANCI DA CINIKAYYA DA YAWON BUDE IDO (COMMERCE, TRADE & TOURISM

Babbar Manufa:
Karfafa ƙananan kasuwanci, faɗaɗa cinikayya, da mayar da Gombe babbar cibiyar kasuwanci a Arewacin Najeriya bayan Kano.

5.1 Raya Kasuwanci da Bada Tallafi

- Asusun Tallafin ’Yan Kasuwa: Za mu haɗa gwiwa da Bank of Industry da SMEDAN domin samar da rance mai juyawa ga ƙananan ’yan kasuwa, matan kasuwa da masu ƙananan sana’o’i, baya ga Asusun Kasuwancin Matasa.
- Za mu haɗa gwiwa da kamfanoni masu zaman kansu domin samar da yankunan kasuwanci da manyan shaguna na zamani a birnin Gombe da manyan garuruwa.

5.2 Sabunta Kasuwanni

- Za mu zamanantar da Babbar Kasuwar Gombe, Tsohuwar Kasuwar Gombe, Kasuwar Tike da kasuwar zamani guda ɗaya a kowace shiyyar sanata.
- Baya ga sabon fasali, kasuwannin za su samu tsaftataccen ruwa, bandakuna masu kyau, wuraren zubar da shara, fitilun tsaro, kayan kashe gobara da sassan kayan da ke saurin lalacewa masu ajiya mai sanyi da wutar hasken rana.

5.3 One-Stop Business Registration Desk

- Za mu ƙarfafa GOSIPA da GIRS domin kammala rijistar kasuwanci cikin sa’o’i 48.
- Za mu samar da fom guda ɗaya, ofishi guda ɗaya da jadawalin kuɗaɗe guda ɗaya domin dukkan rijistar kasuwanci.
- Za mu ba da shawarwari kyauta kan bin dokokin haraji, tsara kasuwanci da samun rance.



Zuwa 2031:

- Za mu tallafa wa aƙalla ƙanana da matsakaitan kamfanoni 50,000 a sarrafa amfanin gona, masana'antu, kasuwancin mata, sababbin kasuwancin matasa da sana'o'in hannu.
- Za mu tabbatar da cewa aƙalla kashi 40% na kamfanonin da aka tallafa mata ne ke jagoranta, kuma aƙalla kashi 35% matasa ne ke jagoranta.
- Za mu wallafa sakamakon shekara-shekara kan kuɗin da aka bayar, biyan rance, dorewar kamfanoni, ƙaruwar kuɗin shiga da ayyukan yi.

5.4 Raya Yawon Buɗe Ido, Al'adu da Karɓar Baƙi

Babbar manufa:

Mayar da Jihar Gombe babbar cibiyar nishaɗi, taruka, yawon buɗe ido na muhalli da al'adu a Arewa maso Gabashin Najeriya.

Our Commitments

- Za mu tsara kuma mu aiwatar da cikakken Babban Tsarin Yawon Buɗe Ido da Karɓar Baƙi na Jihar Gombe domin gano, karewa, raya da tallata albarkatun yawon buɗe ido.
- Za mu mayar da Cibiyar Taron Kasa da Kasa ta Gombe (GICC) babbar cibiyar taruka da bukukuwa a Arewa maso Gabas, ta haɗin gwiwa, ƙwararren gudanarwa da tallata wurin.
- Za mu saukaka gina otel mai taurari biyar, ƙauyen taruka da wurin shakatawa a hanyar GICC zuwa filin jirgin sama domin jawo taruka, baje-koli, 'yan kasuwa, masu zuba jari da masu yawon buɗe ido.
- Za mu raya hanyar tattalin arziki tsakanin Filin Jirgin Sama na Gombe da GICC zuwa yankin otel-otel, nishaɗi da zuba jari, mai gidajen abinci, shaguna, wuraren shakatawa da filayen jama'a masu kyau.
- Za mu inganta Gombe International Hotel, Jewel Hotel Gombe da Kaltungo Jewel Hotel ta hadin gwiwar gwamnati da kamfanoni domin ɗaga matsayin masauki, taruka, nishaɗi da hidimar baki.
- Za mu ƙarfafa faɗaɗa otel-otel a manyan garuruwa da wuraren yawon buɗe ido domin samun masauki mai inganci.
- Za mu inganta Madatsar Dadin Kowa zuwa babbar cibiyar yawon buɗe ido da nishaɗi, mai wuraren bakin ruwa, yawon jirgin ruwa, bukukuwan kamun kifi, wuraren kallo, wuraren cin abinci a waje, masaukai masu kula da muhalli da wuraren nishaɗin iyali.



- Za mu tallata tsaunukan Tangale, Kilang, Kalam da Bima, Kwarin Cham da sauran wurare masu kyan gani domin hawa tsaunuka, ɗaukar hotuna da koyon muhalli.
- Za mu kare da tallata al'adun Masarautar Gombe da al'ummomin Tangale, Tula, Waja, Tera, Bolewa, Fulani da sauransu ta ƙauyukan al'adu, gidajen tarihi, bukukuwa, gine-ginen gargajiya da yawon buɗe ido na tarihi.
- Za mu kafa kalandar bukukuwan yawon buɗe ido da al'adu ta Gombe ta kowace shekara, da hawan doki, zane-zane, sana'o'in hannu, kiɗa, abinci, wasanni da baje-koli.
- Za mu tallafa wa kasuwancin yawon buɗe ido na al'umma, ciki har da jagororin yawon buɗe ido, masu sana'o'in hannu, masu wasan al'adu, masu sufuri, masu shirya taruka, masu ɗaukar hoto da masu karɓar baƙi.
- Za mu ƙirƙiri shirin "Ziyarci Gombe" domin tallata jihar a Najeriya da duniya a matsayin "Lu'ulu'un Savannah", ta dandamalin dijital da haɗin gwiwar yawon buɗe ido.
- Za mu haɗa gwiwa da masu zuba jari wajen gina wuraren hutawa masu kula da muhalli, ƙauyukan hutu, wuraren namun daji, wuraren wasanni da wuraren shakatawar iyali a wuraren da suka dace.
- Za mu kafa shirye-shiryen horon karɓar baƙi da yawon buɗe ido ta makarantun fasaha da sana'a, domin koyar da gudanar da otel, girki, shirya taruka, gudanar da yawon buɗe ido da tallata wurare.
- Za mu tabbatar da ingantattun tituna, tsaro, tsafta, kiyaye muhalli, intanet da agajin gaggawa a manyan wuraren yawon buɗe ido.

5.5 Manufofin Yawon Buɗe Ido

- Za mu jawo aƙalla baƙi **250,000** daga gida da ƙasashen waje a kowace shekara zuwa 2031.
- Za mu samar da aƙalla babban aikin yawon buɗe ido guda ɗaya a kowace shiyyar sanata.
- Za mu jawo gagarumin jarin kamfanoni cikin otel-otel, wuraren hutawa, nishaɗi da taruka.
- Za mu samar da ayyukan yi **20,000** kai tsaye da na kaikaice a yawon buɗe ido, karɓar baƙi, sufuri, zane-zane, nishaɗi, abinci da al'adu.
- Za mu sanya Gombe cikin manyan wurare biyar na taruka, nishaɗi da yawon buɗe ido na muhalli a Arewacin Najeriya.



5.5 Manufofin Samar da Ayyukan Yi

- Za mu samar da sabbin ayyukan yi 100,000 na ainihi a dukkan fannoni cikin shekaru huɗu.
- Za mu samar da aƙalla ayyukan yi 50,000 kai tsaye da na kaikaice a kasuwanci, cinikayya, yawon buɗe ido, karɓar baƙi, sufuri, zane-zane, al'adu, nishaɗi da sauran hidimomi.
- Za mu samar da ayyukan yi ta ingantawa da faɗaɗa Gombe International Hotel, Jewel Hotel Gombe, Kaltungo Jewel Hotel, da gina otel mai taurari biyar, ƙauyen taruka da wurin shakatawa a GICC da hanyar tattalin arziki ta Filin Jirgin Sama–GICC.
- Za mu tallafa wa ayyukan yi ga manajojin otel, ma'aikatan karɓar baƙi, masu girki, masu yawon buɗe ido, masu shirya taruka, masu sana'o'in hannu, masu wasan kwaikwayo, masu ɗaukar hoto da masu sufuri.
- Za mu tallafa wa ayyukan yi ga ƙananan 'yan kasuwa, matan kasuwa da matasa masu sana'o'in ƙirƙira.
- Za mu bunƙasa ƙananan kamfanoni ta Asusun Tallafin 'Yan Kasuwa, Asusun Kasuwancin Matasa da shirye-shiryen haɗin gwiwar kuɗi domin ayyukan yi masu ɗorewa a dukkan LCDAs.
- Za mu samar da ayyukan yi ta sabunta kasuwanni, manyan shaguna, yankunan kasuwanci da cibiyoyin kasuwanci a jihar.
- Za mu samar da ayyukan yi ta wuraren yawon buɗe ido, al'adu, otel-otel, cibiyoyin taruka, wuraren shakatawa da kasuwancin yawon buɗe ido na al'umma.
- Za mu jawo jarin kamfanoni da ke samar da ayyukan yi masu ɗorewa a kasuwanci, yawon buɗe ido, karɓar baƙi da sarƙokin hidimomi.
- Za mu bai wa matasa, mata da masu nakasa fifiko.



GINSHIKI NA 6: FASAHAR ZAMANI DA DAMAR DIJITAL GA KOWA (TECHNOLOGY & DIGITAL INCLUSION)

Babbar Manufa:
Gombe da ba ta rungumi fasahar dijital ba za ta kasance a baya.

6.1 Haɗin Intanet da Faɗaɗa Broadband

- Za mu kai intanet mai sauri ga dukkan LCDAs ta haɗin gwiwar gwamnati da kamfanoni.
- Za mu samar da Wi-Fi kyauta a zaɓaɓbun wuraren shakatawa, kasuwanni, tashoshin mota, asibitoci da muhimman wuraren jama'a.
- Za mu ƙarfafa amfani da hanyoyin biyan kuɗi na dijital a cinikayyar yau da kullum.

6.2 Horar da Matasa a kan Kwarewar Dijital

- Za mu kafa G-ODA (Gombe Digital Opportunities and Advancement) a matsayin babban shirin jihar na horar da ƙwarewar dijital da samar da ayyukan yi.
- G-ODA za ta kasance babbar cibiyar tsara ƙa'idoji, tantance abokan horo da haɗa ƙaramar cibiyar dijital guda ɗaya a kowace shiyyar sanata.
- Za ta haɗa masu horo da ayyukan yi masu albashi da tallafin kasuwanci, ta riƙe rajistar masu cin gajiyar shirin guda ɗaya, kuma ta wallafa sakamako a kowane kwata.
- Ta G-ODA da shirye-shiryen abokan hulɗa, za mu horar da aƙalla matasa 150,000 zuwa 2030 a rubuta manhajoji, ƙirar hoto, tallan dijital, shigarwa da nazarin bayanai, kasuwancin intanet, gudanar da kasuwanci ta yanar gizo da sauran ƙwarewar da ke kaiwa ga ayyukan yi.
- Za mu haɗa matasa da damar yin aiki daga nesa a Najeriya da ƙasashen waje.

Zuwa 2031:

- ▶ Za mu horar da aƙalla matasa 150,000 tare da tallafa wa aƙalla tabbatattun damar samun kuɗin shiga ta dijital 100,000, ciki har da aikin yi, aikin kwangila na kai, aikin sababbin kamfanoni da sauran hanyoyin samun kuɗi.
- ▶ Ayyukan yi masu albashi da aka tabbatar da su da sana'o'in dogaro da kai masu ɗorewa ne kaɗai za a lissafta cikin manufar sabbin ayyukan yi 100,000.



- Za mu ba da rahoton sauran damar samun kuɗin shiga daban, ta rahoton kwata-kwata da zai bambanta adadin mutane na musamman, kammala horo, takardun shaida, samun aiki mai albashi, kafa kasuwanci, wurin zama da shigar mata, domin kauce wa maimaita lissafi.

6.3 Tsarin Gwamnati ta Dijital da Bawa Mutane Dama

- Za mu ƙirƙiri babbar tashar hidimomin gwamnati ta intanet da hanyoyin wayar hannu domin neman takardun fili, izinin kasuwanci, hidimar haraji da sauran ayyukan da ake yawan nema, tare da bibiyar buƙata da sanarwar matsayinta.
- Za mu wallafa kasafin kuɗi, sanarwar sayayya, kwangiloli, wuraren ayyuka, matakin kammalawa, kashe kuɗi da hotuna da aka tabbatar da su a tsarin bibiyar ayyuka na jama'a.
- Za mu ba jama'a damar aika korafe-korafe, buƙatun hidima, shawarwari da hujjoji ta tashar intanet, SMS, USSD, cibiyoyin kira da ofisoshin taimako, tare da lambobin bibiyar ƙorafi da wa'adin amsa.
- Za mu yi amfani da tattaunawar intanet, jin ra'ayin jama'a, tsara kasafi tare da jama'a da tarukan gari na dijital domin karɓar shawarwari kan kasafi, manufofi, ayyuka da hidimomin gida kafin manyan shawarwari.
- Za mu samar da taimakon samun hidima a ofisoshin LCDAs da cibiyoyin dijital ga waɗanda ba su da wayar zamani, intanet ko ƙwarewar dijital, tare da hanyoyin da masu nakasa za su iya amfani da su.
- Za mu wallafa rahoton shiga da ra'ayin jama'a a kowane kwata, wanda zai nuna buƙatun da aka karɓa, matsalolin da aka warware, lokacin amsawa, sakamakon tattaunawa da yadda ra'ayin jama'a ya sauya shawarar gwamnati.

6.4 Tallata Yawon Buɗe Ido ta Dijital

- Za mu gina dandamalin "Ziyarci Gombe" na dijital wanda zai nuna wuraren yawon buɗe ido, otel-otel, taruka, hanyoyin sufuri da bayanan baƙi.
- Za mu gudanar da kamfen na tallata wurare ta dijital domin jawo masu zuwa taruka, nishaɗi da yawon buɗe ido na muhalli.
- Za mu tallafa wa kasuwancin yawon buɗe ido da tsarin biyan kuɗi na dijital, yin ajiyar wuri ta intanet da kasuwancin yanar gizo.



6.4 Fasahar Zamani a Fannin Ilimi



- Za mu aiwatar da Shirin Ilimin Dijital na Gombe daga Firamare 1 zuwa JSS 3 tare da kamfanonin fasaha, ƙungiyoyin raya ƙasa da ƙungiyoyi masu zaman kansu, ta samar da darussan dijital masu dacewa da shekaru, tushen amfani da kwamfuta, tsaron intanet da kayan koyon aiki.
- Za mu kafa da samar da kayan aiki a cibiyoyin ilimin dijital a makarantun sakandaren gwamnati, tare da fifita yankunan da ba su samu isassun hidimomi ba da wuraren da masu nakasa za su iya shiga.
- Za mu horar da malamai kan amfani da kayan dijital wajen koyarwa, tare da ba makarantu ingantaccen intanet, na'urorin haɗin gwiwa, tallafin fasaha, kula da kayan aiki da ƙa'idojin kare yara a intanet.
- Zuwa 2031, za mu cim ma kashi 90% na ƙwarewar dijital a makarantun firamare da sakandaren gwamnati, tare da rahoton shekara-shekara kan makarantu masu intanet, cibiyoyi masu aiki, malamai da aka horar, ɗaliban da aka kai wa, ingancin na'urori da ƙwarewar da aka tantance.





GINSHIKI NA 7: TSARO DA MUHALLI

Babbar Manufa:
No security without environmental healing. No environmental sustainability without security.

7.1 Matakan Tsaro a Matsayin Tushen Ci Gaba

- Za mu tallafa wa gyare-gyaren tsaro da kundin tsarin mulki ya amince da su domin ƙarfafa aikin ’yan sanda a matakin jiha da al’umma, tare da sarakunan gargajiya, ƙungiyoyin tsaron al’umma da hukumomin tsaro na tarayya.
- Za mu kafa majalisun sulhun manoma da makiyaya a kowace LCDA.
- Za mu ƙarfafa tsaron kan iyakoki ta sintiri, bayanan sirri da haɗin gwiwa da maƙwabta.
- Za mu yi amfani da horo, ayyukan yi da kasuwanci ga matasa a matsayin dabarar tsaro.
- Za mu ƙarfafa tsaro da agajin gaggawa a wuraren yawon buɗe ido, taruka, otel-otel da nishaɗi.

7.2 Jami’an Kare Muhalli

- Za mu horar da jami’an kare muhalli da masu gadin daji 1,000 daga al’ummomi, tare da kayan aiki da tallafin hukumomin tsaro.
- Aikinsu shi ne kare dazuzzuka, wuraren tattara ruwa da wuraren kiwo daga sare bishiyoyi ba bisa ka’ida ba, ƙone daji da mamaye ƙasa.



7.3 Alaƙar Tsaro da Muhalli

Sare Dazuzzuka

- Matsalar tsaro: Karancin ƙasa, ciyawar kiwo da itacen girki na iya ƙara talauci, rikicin manoma da makiyaya da laifuka a karkara.
- Mafita: Maido da dazuzzuka ta kula da al'umma, dasa bishiyoyi da sa ido kan rayuwarsu, jami'an muhalli da wasu hanyoyin samun kuɗin shiga masu ɗorewa.

Lalacewar Kasa

- Matsalar tsaro: Raguwar amfanin gona da kiwo na ƙara ƙarancin abinci, ƙaura da gasa kan ƙasa da ruwa.
- Mafita: Gyara gonaki da wuraren kiwo ta kiyaye ƙasa, dasa ciyawa, wuraren ruwa da bankunan ajiyar abincin dabbobi.

Zaizayar Kasa

- Matsalar tsaro: Lalacewar gidaje, tituna, gonaki da hanyoyin ruwa na tilasta ƙaura, ware al'ummomi da haifar da takaddama kan ƙasa mai aminci.
- Mafita: Magudanan ruwa, daidaita ƙasa, kare wuraren da bai kamata a gina ba da tsarin gargaɗin al'umma.

Fari da Rashin Amfanin Gona

- Matsalar tsaro: Asarar amfanin gona da dabbobi na haifar da yunwa, rashin abinci mai gina jiki, ƙaura ta dole, rashin aikin yi da tashin hankali.
- Mafita: Faɗaɗa ban-ruwa, tara ruwan sama, amfanin gona masu jure fari, inshorar noma, tallafin abinci da ayyukan yi na karkara masu dacewa da yanayi.

7.4 Maido da Dazuzzuka da Dashen Bishiyoyi

- Za mu farfaɗo da shirin Gombe Goes Green (3G): dasa bishiyoyi miliyan huɗu cikin shekaru huɗu, tare da sa ido kan waɗanda suka rayu.
- Za mu ƙaddamar da tsarin mallakar bishiya ga gidaje, makarantu, cibiyoyin addini da gonaki.
- Za mu kafa layukan bishiyoyin kariya daga iska da hamada a arewacin jihar.
- Za mu jawo kuɗaɗen green bonds da tallafin kasuwar carbon domin ayyukan da suka dace da sauyin yanayi.
- Za mu raya zaɓaɓbun gandun daji da wuraren da aka kare muhalli domin yawon buɗe ido, taruka, otel-otel da nishaɗi.



7.5 Yaƙi da Hamada da Lalacewar Ƙasa

- Za mu horar da manoma kan sarrafa ƙasa mai ɗorewa, kamar sauya irin amfanin gona, rufe ƙasa da tarkacen tsire-tsire da noman bin gangara.
- Za mu rage yawo da dabbobi ba tare da tsayayyen wuri ba ta farfaɗo da wuraren kiwo masu ruwa da ajiyar abincin dabbobi.
- Za mu gyara ƙasashen da suka lalace ta matakan ƙasa, katangun riƙe ƙasa da dasa ciyawa.

7.6 Yaƙi da Zaizayar Kasa da Ambaliyan Ruwa

- Za mu kammala dukkan ayyukan yaƙi da manyan ramukan zaizayar ƙasa da ake yi, mu kuma fara sababbi.
- Za mu kafa tashoshin lura da yanayi na gida da tsarin gargaɗin wuri tare da NIMET.
- Za mu gano wuraren da ke cikin haɗari kuma mu aiwatar da dokokin kiyaye tazara a bakin koguna da fadamu.

7.7 Kula da Shara da Hana Gurɓata Muhalli

- Za mu kafa cibiyoyin tantance kayan shara da masana'antun sake sarrafa roba, takarda, gilashi da ƙarafa.
- Za mu tsara harkar tattara tsofaffin ƙarafa da shara ta rajista, wuraren tara kaya, ƙa'idojin tsaron ma'aikata da hukunci kan sata, sarrafa kaya ba cikin aminci ba da gurɓata muhalli.
- Za mu ci gaba da tsaftar muhalli ta al'umma a kowane wata, tare da ba da kyaututtuka ga LCDAs, mazabu da kasuwanni mafi tsafta.
- Za mu tabbatar da ƙa'idojin muhalli a wuraren yawon buɗe ido, otel-otel, taruka da nishaɗi.

7.8 Daidaitawa da Sauyin Yanayi da Hanyoyin Rayuwa Masu Juriya

- Noma mai dacewa da sauyin yanayi: Zuwa 2031, za mu gudanar da gonar gwaji guda ɗaya a kowace LCDA, tare da tura jami'an faɗakarwa 300 domin koyar da amfanin gona masu jure fari, tara ruwa, kiyaye ƙasa, ingantaccen ban-ruwa da shuka bisa bayanan yanayi.
- Jagora: Ma'aikatar Noma. Masu tallafi: Ma'aikatun Muhalli da Albarkatun Ruwa.
- Maido da ƙasa da hanyoyin samun kuɗin shiga: Za mu gyara gonaki da wuraren kiwo da suka lalace ta dasa ciyawa, ajiyar abincin dabbobi, wuraren ruwa, layukan bishiyoyin kariya da tsarin mallakar bishiya na al'umma. Wannan zai taimaka wa burin bishiyoyi miliyan huɗu da rage matsin lamba kan ƙasa, kiwo da itacen girki.



- Jagora: Ma'aikatun Muhalli da Raya Kiwo. Masu tallafi: LCDAs da cibiyoyin al'umma.
- Jure ambaliya da zaizayar ƙasa: Zuwa 2031, za mu yi taswirar dukkan manyan wuraren haɗari, mu gyara aƙalla ramukan zaizayar ƙasa 10 masu tsanani, mu farfaɗo da manyan magudanan ruwa 20, kuma mu rage maimaituwar lalacewar muhimman kadarorin jama'a da aƙalla kashi 30%.
- Jagora: Ma'aikatar Muhalli. Masu tallafi: GOSUPDA, Albarkatun Ruwa, Ayyuka, SEMA, LCDAs da NIMET.
- Kariya daga fari da ƙarancin abinci: Za mu gwada inshorar noma mai araha da biyan diyya bisa alamomin yanayi ko yawan amfanin gona a al'ummomin da ke cikin haɗari, tare da fifita ƙananan manoma, mata, matasa da masu kiwo.
- Za mu wallafa rahoton shekara-shekara kan manoman da aka rufe da inshora, bukatun diyya, kuɗin da aka biya, gonakin ban-ruwa, asarar amfanin gona da farfaɗowar hanyoyin samun kuɗin shiga.
- Jagora: Ma'aikatar Noma. Masu tallafi: Ma'aikatun Kuɗi, Raya Kiwo da Agajin Jinƙai, tare da kamfanonin inshora da abokan raya ƙasa.



FALSAFAR GUDANAR DA MULKINMU

01

Bin Diddigi

A kowace shekara, za mu wallafa rahoton auna ayyukanmu ga jama'a: abin da muka yi alƙawari, abin da muka aiwatar da abin da ya rage.

02

Ci Gaba da Ayyukan da Aka Fara

Za mu kare, kammala da faɗaɗa kyawawan ayyukan Gwamna Inuwa Yahaya. Ba za mu rusa abin da yake aiki ba. Ba za mu yi iƙirarin fara komai daga tushe ba alhali an riga an kafa ginshiƙi.

03

Gudanar da Kuɗaɗen Jama'a Cikin Amana

Gwamna Inuwa Yahaya ya kafa Jihar Gombe a kan tubalin kuɗi mai ƙarfi, bisa taka-tsantsan da tsauraran ƙa'idojin yin hisabi. Ko da yake wuce wannan mataki ba abu ne mai sauƙi ba, za mu yi ƙoƙarin kiyaye shi, hana kashe kuɗi ba bisa ƙa'ida ba, da tabbatar da cewa kowace naira tana samar wa jama'a amfani mai ɗorewa.

04

Tafiya da Kowa

Ba za a bar wani mutum ko al'umma a baya ba saboda wurin zama, jinsi, ƙabila, addini ko matsayin zamantakewa. Gwamnatinmu za ta wakilci dukkan bambancin al'ummar Gombe.





TSARINMU NA BIN DIDDIGI

Ba ma neman a amince da mu ba tare da tambaya ba; muna neman yarjejeniya da aka gina a cikinta tsarin yin hisabi.

01

Tsarin Nuna Matakin Ayyuka

Za a nuna kowane babban aiki, wurinsa, kasafinsa, ɗan kwangila, kaso na kammalawa da hotunansa.

02

Rahoton Aiwatar da Kasafin Kuɗi

Za mu bayyana abin da aka ware a kasafi, abin da aka kashe da abin da aka cim ma.

03

Tsarin Bibiyar Ci Gaban Manufofin Kawo Sauyi Mai Inganci

Za a nuna matsayin kowane alƙawari daga cikin waɗanda aka bayyana a sama: Ba a Fara ba; Ana Aiki; An Kammala; ko An Samu Jinkiri.

04

Rahotannin Kuɗi da Aka Tantance

Za a wallafa rahotannin kuɗi da aka yi wa binciken masu tantance kuɗi, a gabatar da su ga jama'a cikin wa'adin da doka ta tanada.

05

Rahoton Ra'ayoyi da Korafe-korafen Jama'a

Za a bayyana korafe-korafen da aka karba, aka bincika da waɗanda aka warware.



Domin Ingantacciyar Jihar Gombe.

A GREATER GOMBE TOGETHER

ALƘAWARINA NA KAINA



RENEWED Hope 2.0

Zan gudanar da kuɗaɗen jama'a cikin gaskiya, yin hisabi da taka-tsantsan.
Zan kasance shugaba mai sauraron jama'a: zan saurari talaka da mai arziki, waɗanda suka zaɓe ni da waɗanda ba su zaɓe ni ba.
Zan yi mulki cikin adalci da gaskiya, in tafi da kowa ba tare da la'akari da addini, ƙabila ko jam'iyyar siyasa ba.
Zan yi aiki tuƙuru domin in bar Gombe cikin yanayi mafi kyau fiye da yadda na same ta.

KAMMALAWA

Wannan kundin manufofi ba takardar yakin neman zabe ba ce da za a karanta, a yaba, sannan a manta. An rubuta shi da harshe mai sauki domin kowa ya fahimta. Mun fayyace alkawuranmu domin kowa ya iya tantance cika su.

YANZU MUN GABATAR DA SHI A GABANKU.

KU KARANTA SHI. KU TATTAUNA SHI. KU YI TAMBAYOYI.

KU BA NI AMANAR SHUGABANCI. NI KUMA ZAN SADAUKAR DA DUKKAN KARFINA.



KU ZAƁI CI GABA DA ZAMAN LAFIYA!



Dr. Jamil Isyaku
GWAMNA
(Sardaunan Gombe)

TARE DON
GINA GOMBE
MAFI GIRMA

JAMA'A,
DAMA
DA WADATA.

KU YI ZAƁE CIKIN HIKIMA!



RENEWED Hope 2.0

KU ZAƁI SARDAUNAN GOMBE!

KU ZAƁI CI GABA DA ZAMAN LAFIYA!

KUNGIYAR YAKIN NEMAN ZAƁEN JAMIL GWAMNA

AN KIYAYE DUKKAN HAKKOKI
© 2026